*HAUSA HEART Book*

# ZUCIYAR MUTUM



**COPYRIGHT**
**ISBN 0 - 908412 - 46 - 0**

**E-MAIL: info@angp.co.za**
**ALL NATIONS GOSPEL PUBLISHERS**
**Posbus 2191, PRETORIA, 0001, R.S.A.**

Copyright ANGP

(A Gospel Literature Mission financed by donations)
(Reg. No. 1961/001798/08)

**Zuciyar Mutum**
**Gidan Allah ko kuwa Mazaunin Shaiɗan – 1 Yoh. 3:410.**

Wannan littafi ba wani sabon labari ba ne. Aka fara rubuta shi a ƙasar Faransai tun dā. Ya yi wa mutane da yawa taimako. Ya zama kamar madubi inda mutane su ke ganin yadda zukatansu su ke a gaban Allah. Mutane da yawa sun ga zunuban zukatansu, sun kuwa tuba, sun sami sababbin zukata da sabon ruhu.

A cikin karatun wannan littafi ka tuna dai, madubi ne shi inda ka ke ganin kamanninka. Ko marar bi ne kai, ko mai bi ne, ko kuwa wanda ya ja da baya ne, nan za ka ga siffaraka daidai yadda Allah ya ke ganinka. Allah ba ya tarar kowa. Yana duban zuciyar mutum, ba fuskarsa kaɗai ba, ko launin fatarsa.

Shaiɗan uban maƙaryata ne, sarkin duhu ne, shi ne kuma mai mulkin duniya. Ya kan mai da kansa kamar mala'ikan haske ne. Mutane da yawa kuwa su kan karɓe shi a kan haka, amma ba haka ya ke ba. Suna jin haushi sabo da siffofin da su ke bayyana halinsa sosai. Akwai masu ƙaryan manzanci, da wasu ma'aikata masu ha'inci, su kan mai da kansu manzannin Almasihu (2 Kor. 11:13-14). Saiɗan ya kan makantad da idanun mutane da hankalinsu kuma, don kada su gāne da ƙaunar Allah, don kada su ga darajar Allah da ɗaukakarsa kuma, don kada su ga Yesu kuma Mai Fansarsu (2 Kor. 4:4). Waɗanda

Shaiɗan ya makantad da su ba su ga suna halaka suna kuwa faɗuwa cikin Gidan Wuta ta har abada ba. Suna kuwa faɗuwa cikin Gidan Wuta mai ƙonewa da kibritu har abada. Tun suna da ransu matattu ne su a gaban Allah. Shaiɗan ne yana mulke su (Afis. 2:2).

Dalilin bayyanuwar Ɗan Allah ke nan, don ya hallaka ayyukan Shaiɗan (1 Yoh. 3:8). Ku zama fa masu biyayya ga Allah, amma ku yi tsayayya da Shaiɗan, zai fa guje muku. Ku kusato ga Allah, shi kuwa zai kusato gare ku (Yak. 4:7,8).

Tun kana karatun wannan littafi, kana kallon siffofi kuma, sai ka duba cikin zuciyarka, ka bincike ta, ka ga yadda ta ke. Idan ka ga zuciyarka mummuna ce, mai zunubi, kada ka yi musu, kada kuma ka ɓoye laifinka, amma ka yi gaskiya, ka faɗi zunubanka. Idan mun faɗi zunubammu, Allah mai alkawari ne, mai adalci kuma, da zai gafarta mana zunubammu, ya tsarkake mu daga dukan rashin adalci. Idan mun ce ba mu yi zunubi ba, muna maishe shi maƙaryaci, kuma magana tasa ba ta cikimmiu (1 Yoh. 1:9,10). Ku ƙasƙantad da kanku fa ƙarƙashin hannun Allah mai iko, don ya gafarta muku zunubanku, ya tsarkake ku da jini mai daraja na Yesu Almasihu.

Allah ne yana mulkinka, im ba haka ba Shaiɗan ya kan yi. Kai bawan Allah ne, ko kuwa bawan Shaiɗan. Idan zunubi yana mulkin ranka kada ka yi musu, amma sai ka yi roƙo ga Allah. Zai sake halinka ta wurin ikon Yesu, wanda ya zo duniya don ceton masu zunubi. Ya zo ya buɗe idanun makafi don su ga haske, ya fid da su daga cikin duhu, ya fid da duhu kuma daga cikinsu. Yesu ya zo don ya haskaka mu da haskensa. Yesu ya zo domin ya sake mu daga ikon zunubi, da na Shaiɗan kuma. Ya kuwa fanshe mu daga bautar zunubammu. Kana tsaye a gaban Allah wanda ya ke tsattsarka. Yana ganin kome. Ya kuwa san asiranka duka, da ɓoyayyun abubuwa, har da tunanin zuciyarka kuma. Ba zai yiwu ka ɓuya daga fuskar Allah, ko kuwa ka ɓoye ayyukanka ba. Shi wanda ya dasa kunne, ba zai ji ba? Shi wanda ya siffanta ido, ba zai gani ba? (Zab. 94:9). Gama idanunsa suna duban tafarkun mutane. Yana kuwa ganin dukan hanyoyinsu. Babu wani duhu ko inuwar mutuwa, inda masu aikata mugunta za su ɓuya (Ayuba 34:21-22). Gama idanun Ubangiji suna kai da komowa a cikin dukan duniya, domin ya bayyana kansa mai ƙarfi sabo da waɗanda zuciyarsu ta kamalta gare shi (2 Lab. 16:9; Yoh. 2:24).

Mai albarka ne mutum wanda aka gafarta masa laifinsa, wanda aka rufe zunubinsa. Mai albarka ne mutum wanda Ubangiji ba ya lasafta mugunta gare shi, wanda ba shi da algus cikin ruhunsa (Zab. 32:1-5). (Karanta Zab. 51 kuma). Har yau Yesu yana kira cewa, “Ku zo gare ni dukanku da ku ke wahala, masu nauyin kaya kuma, ni kuwa im ba ku hutawa” (Matta 11:28).

Copyright ANGP

## 1. ZUCIYAR MAI ZUNUBI




Wannan siffa tana bayyana zuciyar marar bi, watau ta mai zunubi, ko mace ce, ko namiji ne. Ta nuna mana kuma zuciyar ko wane mutumin duhu inda ya ke duka, watau duk wanda ba a haife shi daga bisa ba. Duniya, da sha'awoyinta, da kwaɗayinta, su kan yi mulkin zuciyarsa. Wannan siffa kwatancin madubi ne inda a ke ganin zuciya daidai yadda Allah ya ke ganinta. Idanun mutumin jajjaye ne, waɗanda ba su da kyau, sabo da shan giya da ya ke yi. Wa ke yin wayyo?… Wa ke da jajjayen idanu? Sai waɗanda su kan daɗe wurin shan ruwan inabi, su masu biɗan damammen ruwan inabi. Kada ka dubi ruwan inabi sa'ad da ya yi ja, sa'ad da ya ke ba da launi cikin ƙoƙo. Sa'ad da ya ke gangarawa da daɗi. A ƙarshe ya kan sare kamar maciji. Ya kan yi harbi kamar kāsa. Idanunka za su duba baƙin al'amura. Zuciyarka za ta furta matsaloli na gautsi (Mis. 23:29-33).

Bayan ka duba kai, idan ka duba ƙasa da shi za ka ga maimakon jiki aka zana kwatancin zuciya da namomi iri iri a ciki. Waɗannan namomi sun zama misalin zunubai iri iri waɗanda su ke cikin zuciyar mutum. Zuciyar marar bi ta zama gidan zunubai ke nan. Allah ya ce, "Zuciya ta fi kome rikici, cuta gare ta ƙwarai, irin ta fid da zuciya, wa zai san ta?" (Irm. 17:9). Yesu da kansa ya ce, "Gama daga ciki, daga cikin zuciyar mutum, miyagun tunani ke fitowa, fasikanci, sata, kisan kai, zina, kwaɗayi, mugunta, ha'inci, mugun guri, maita, zage zage, girman kai, wauta. Dukan waɗannan miyagun abu daga ciki su ke" (Mk. 7:21-23).

**1. Kwaɗo** – Talikin fari kwaɗo ne. Kowa ya san kwaɗo da kumburi, wai don girman kai ne. Yana so ya mai da kansa fiye da matsayinsa. Ya zama misalin zunubin girman kai. Lucifer, cherub na Allah ne a dā, shafaffe, mai ɗaukan hasken Allah, shi mala'ika ne na Allah. Sabo da girman kai ya faɗi, ya zama maƙiyin Allah, watau Shaiɗan. (Ish. 14:917). Amma Shaiɗan ba ya kan bayyana kansa mala'ikan duhu ne ba.

Girman kai yana da hanya dabam dabam. Waɗansu su kan yi girman kai sabo da kuɗinsu, wasu sabo da shanunsu ko tumakinsu. Waɗansu sabo da gidaje da gonaki su kan yi girman kai, waɗansu fa sabo da kyawawan tufafinsu masu daraja. Waɗansu kuma su kan yi girman kai sabo da kyaun fuska, ko kyaun jiki, suna kuwa nuna jikinsu sai ka ce tsirara su ke. Ba su da kunya. Waɗansu su kan yi girman

Copyright ANGP

kai sabo da kabilarsu, ko sabo da ilminsu. Waɗansu suna takama sabo da ƙarfin jikinsu ko ƙoƙarinsu da su ke yi a wannan duniya, waɗansu a kan launin fatarsu ko waɗansu abubuwan banza. Waɗansu kuma su kan sa mandaye da 'yan kunne. Suna yi wa 'ya'yansu zane zane iri iri, don su ƙara kyau. Allah dai ya cika musu kyau tun halittarsu. Allah yana tsayayya da masu girman kai, amma yana ba da alheri ga masu tawali'u (1 Bit. 5:5). Allah yana ƙin girman kai da alfarma. (Mis. 8:13). Bayan girman kai sai halaka, faɗuwa kuma tana biye da ta da hanci (Mis. 16:18).

2. **Kare** – Kare ya zama misalin kwaɗayin jiki, da ƙazanta, da zina da fasikanci. Inda kare ya tafi duka sai ya zama ƙazami. Mutane da yawa fa suna yin hakanan. Fasikanci da zina sun ƙaru ƙwarai a zamanin nan na ƙarshe, mai mugunta. Samari da 'yam mata ba su da haƙuri. Maza da mata masu aure, har da gwauraye da yawa su kan yi zina. Zunubin mutanen Sodom, watau lutsu, ya kama mutane dubbai. An cika annabcin Yesu, inda ya ce a kwanakin ƙarshe mutane za su zama kamar na Sodom da Gomorrah. Waɗansu kabilu suna ce da mazinata karnuka. Irin waɗannan ba za su shiga mulkin Allah ba. Daga waje da karnuka, da masu sihiri, da fasikai, da masu kisan kai, da masu bautan gumaka, da dukan wanda ya ke ƙaunar ƙarya yana kuwa aikata ta (Ruya 22:15). Sabo da haka sai ku guje wa fasikanci. Ko wane zunubin da mutum ya ke yi na bayan jiki ne, amma mai aikin fasikanci yana yi wa jikinsa zunubi. Ko ba ku sani ba ikinku haikali ne na Ruhu Tsattsarka wanda ke cikinku? (1 Kor. 6:18-20).

Idan kowa (mace ko namiji) ya ɓata haikalin Allah, Allah zai ɓata shi, gama haikalin Allah Mai Tsarki ne, watau ku ne (1 Kor. 3:17).

Copyright ANGP

3. **Alade** – Alade ya zama misalin zunubin da ke cikin shan giya da zarin ci. Alade-ya kan ci kome. Ya kan ci mai kyau ko ruɓaɓɓe. Haka fa waɗansu mutane suna cin abubuwan da Allah ya ce kada a ci. Suna cin mushe. Suna cin nama wanda ba a yanke don jini ya fita ba. Suna shan jini (A.M. 15:20; Ish 66:3-7). Ban da wannan kuma su kan ɓata jikinsu ta wurin shan taba. Shaiɗan yana ɗaure su da sarƙar shan taba. Sai ta wurin ikon Allah a ke yanke wannan sarƙar mai ƙazanta. Tsofaffi duk da samari da 'yam mata su kan yi hauka wurin shan giya, da bammi, da barasa. Masu maye ba za su gaji mulkin Allah ba. Giya ba abinci ba ne, dafi ne mai ɓata hankalin masu sha. Ta kan sa mashaya su yi wauta, ta sa su yi fasikanci, har su yi kisan kai. Ba abin da ba su yi ba sabo da wannan hauka. Ruwan inabi mai ba'a ne, barasa kuma mai tankiya ce. Dukan wanda ya saɓa ta wurinta marar hikima ne (Mis. 20:1). Musa ya rubuta cikin Attaura, ya ce, "Idan… mutum yana da ɗa kangararre ne, …mashayi ne kuma, sai … su jajjefe shi da duwatsu, har ya mutu" (Kub. S. 21:18-21). Waɗanda su ka dafa giya da sauran makamancinta, da mai sayarwa, da wanda ya ke sha, alhakinsu ɗaya ne. Maganar Allah ta ce, "Kaiton waɗanda su ke da ƙarfi wajen shan ruwan inabi, ƙarfafan mutane ga wajen surkan barasa" (Ish 5:22). Kaitonsa shi wanda ke ba maƙwaucinsa sha, kana ƙara naka dafi gare shi, kana kuwa sa shi ya yi maye (Hab. 2:15). Kada ku yaudaru; da masu fasikanci, da masu bautan gumaka, da mazinata, da baran mata, da masu kwana da maza, da ɓarayi, da masu ƙyashi, da masu maye, da masu alfasha, da masu ƙwace, ba za su gaji mulkin Allah ba (1 Kor. 6:9-10).

Ayyukan jiki fa a bayyane su ke, bautar gumaka, sihiri, magautaka, husuma, kishe kishe, … rabuwa, hamayya, … nishaɗai da irin waɗannan. Ina kuwa faɗakad da ku, … su waɗanda ke aikata waɗannan al'amura ba za su gaji mulkin Allah ba (Gal. 5:19-21). Kada ku yi maye da ruwan inabi kuma (watau bammin da a ke yi da shi) cikinsa da hauka, amma ku cika da Ruhu (Afis. 5:18). Ga mai jin kishi, Yesu mabulbulan ruwa na rai yana kira, cewa, "Idan ko wane mutum yana jin ƙishi ya zo gare ni, ya sha ruwa na rai kyauta" (Yoh. 7:37,38). Ya ku, ko wane ɗayanku mai jin ƙishi, ku zo wurin ruwaye, har da shi wanda ba shi da kuɗi. Ku zo ku saya, ku ci, i, ku zo ku sayi ruwan inabi da madara ba da kuɗi, ba da abin biya ba. Dom me ku ke awon abin da ba abinci ba ne? kuna ɓarnatad da hakkinku domin abin da bai sa ƙoshi ba? (Ish. 55:1-2).

4. **Kunkuru** – Naman nan wanda ba shi da zafin tafiya ya zama misalin zunubin da ke cikin ragwanci, da rashin ban gaskiya, da sihiri. Rashin ban gaskiya ya zama kamar zunubin da ya ke cikin sihiri. Raggo ya kan shiga cikin tarko da jarabobi da yawa. Sata ta fi aiki araha a gare shi. Sata fa ta kan haifi kisan kai. Ragwanci ya kan hana mana yin addu'a, da karatun Littafi Mai tsarki, da zuwa majam'a. Ya kan hana mana binciken Maganar Allah, inda a ke nuna mana hanyar rai na har abada. Ragwanci ya kan hana wa mutane masu jin Maganar Allah su ba da gaskiya. Sabo da haka ragwanci ya kan kai su ga halaka. A lokacin da Allah ya ke magana da zuciyarka cewa, ka ba shi gaskiya, sai Shaiɗan ya shiga ya ce, "Kada ka yi yau". Yana so ka jira zuwa gobe, ko ran da ka sami zarafi. Assha! Ran nan mai zarafi ba ta zuwa. Ragwancin nan yana hana maka ba da gaskiya yau da gobe, bana ba baɗi, sai mutuwa ta yanke maka zarafi. In haka ne za ka fita duniya ba Allah, ba ceto, ba Almasihu. Sabo da haka Allah ya ce, "Yao kadan kun ji murya tasa, kada ku taurare zukatanku" (Ibr. 3:7-8).

Bokaye su kan yi magani da ƙoƙon kunkuru. Sabo da wannan fa ƙoƙon nan ya zama misalin zunubin da ya ke cikin dogara ga bokanci da sihiri, ba ga Allah Mai Rai ba. A lokacin da mutane su ke wahala ko rashin lafiya, maimakon addu'a ga Allah, su kan dogara ga gumaka, da saiwoyi, da duwatsu, da ƙahoni, da sauran magungunan bokaye. Abin da ya kamata fa su dogara ga Mahaliccinsu da Mai Fansarsu. Allah ya dokaci Isra'ilawa cewa, "Ba za ka bar mayya ta rayu ba" (watau mai sihiri) (Fit. 22:18). Daga cikinku ba za a iske wanda ya ke … yin istihara, ko mai yin duba, ko mai waibuwa, ko mai sihiri, ko mai arwa, ko mai magana da mai mabiya, ko mai maita, ko mai sha'ani da matattu. Gama wanda ya aikata waɗannan al'amura duka abin ƙyama ne ga Ubangiji (Kub. S. 18:10-12). Kada ku bi wurin masu mabiya, ko kuwa wurin mayu. Kada ku neme su, don kada ku ƙazantu ta wurinsu. Ni ne Ubangiji Allahnku (Lev. 19:31). Mutum kuma wanda ya tafi wurin masu mabiya, da wurin mayu, don ya bi su cikin karuwanci, sai in la'anta wannan mutum, in datse shi daga cikin jama'arsa. Ku tsarkake kanku fa, ku zama masu tsarki, gama ni ne Ubangiji Allahnku (Lev. 20:6,7). Yesu Almasihu kaɗai ya iya warkad da ruhu, da rai, da jiki, shi ne ya kan gafarta dukan laifofinka, ya kuwa warkad da dukan cutanka (Zab. 103:1-3). Akwai mai ciwo a cikinku? Sai ya kira dattijan ekklesiya (ba bokwaye ba) su yi addu'a a bisansa, suna shafe shi da mai cikin sunan Ubangiji. Addu'ar ban gaskiya kuwa za ta ceci mai ciwo, Ubangiji kuwa zai tashe shi. Idan kuma ya yi zunubai, za a gafarta masa (Yak. 5:14-15).

Copyright ANGP

Tun kana karatun wannan ɗan littafi, Allah yana magana da kai cewa, "Ka tuba, ka bar zunubanka, ka ba da gaskiya gare ni." Amma halin kunkuru da ya ke cikin zuciyarka yana raɗa a kunnenka cewa, "kada ka yi gaggawa, kada ka ba da gaskiya yau, sai gobe, ko bakwai mai zuwa, ko baɗi." Ya kan ce wa mata, "Ki yi shawara da mijinki tukuna, sai ki tambayi ubanki tukuna, bari sai kin yi aure tukuna." Kana ƙin biyayya ga muryar Allah ke nan, kana saurarin muryar Shaiɗan mai ruɗi. Ta haka ka ke taurara zuciyarka, sai ta zama kamar ƙoƙon kunkuru.

5. **Damisa** – Damisa mugunyar nama ce, mai saurin kisa. Ta zama misalin haushi, da fushi, da hasala waɗanda su ke cikin zuciyar mutum. Mai hasala da mai fushi ba su da tausayi, su kan yi zagi, su kan ambaci sunan Allah banza, har wani lokaci kisan kai su ke yi. Mutane su kan sami wani halin shaiɗanci kuma wurin shan giya da barasa, har ba su iya mulkin kansu ba. Matsorata da yawa su kan sha giya don su sami ƙarfin hali su yi wani mugun aiki, su rama wa wani. Ruwan inabi dafi ne kamar na kāsaye, dafi ne mai zafi irin na kububuwa kuma (Kub. S. 32:33). Ramawa tana da daɗi ga zuciyar mai zunubi, amma Allah kaɗai yana da iznin ramawa. Yesu ya ce, "Ku ƙaunaci magautanku." Allah ya yi alkawari, zai gafarta mana laifofimmu, idan mun gafarta wa waɗanda su ke yi mana laifi.

6. **Maciji –** Tun farko naman nan yana da gwanin ban sha'awa, har lokacin da ya ruɗi Adamu da Hawwa'u a cikin gonar Adnin. Ya ɓata zumunta wadda ta ke tsakaninsu da Allah. Shaiɗan ya ji kishi lokacin da ya ga yadda Allah ya ke ƙaunar mutumin nan da macen nan. Ya ga Allah ya ba su mulkin

duniya maimakonsa. Sabo da kishin nan Shaiɗan ya yi mugun dabara, ya ɓata zumunta wadda ta ke tsakanin mutumin da Allah. Wannan mugun kishi yana cikin zuciyarka. Yana hana maka jin daɗi idan ka ga wani ya fi ka farin ciki ko daɗin zama. Ya kamata ma'aikatan Allah, masu wa'azi, su lura don kada wannan mugun hali na kishi ya same su in sun ga wani ma'aikaci ya fi su samun albarka. Kishi ya kan sa miyagun tunani a cikin zuciyarka, har ka so ka yi wa wani magani, a ɓata masa jin daɗi, ko a kashe shi. Kishi tsakanin mutum da mai ɗakinsa ya kan ɓata zaman gida da dukan harkokinsu. Kishi yana da mugunta kamar kabari (Waƙ. W. 8:6).

**7.** **Kura** – Ba abin da kura ba ta ci. Ta zama misalin kwaɗayi. Gama son kuɗi, da wadata, asalin ko wace irin mugunta ne (1 Tim. 6:10). An taɓa ganin kura ta ci wanda bai mutu ba tukuna, ta kuma ci mushe. Sai ka ce ba ta kan ƙoshi ba. Ta kan ci nama mai kyau, ta kuma ci dafi, ba ta kula ba in ya shiga ciki. Mai kwaɗayi ba ya so ya taimaki matalauta. Yana ƙoƙari iyakar dabararsa ko bisa gaskiya, ko bisa rashin gaskiya, ya tara wadata irin ta duniya, wadda asu da tsatsa ke cinyewa. Yesu ya ce, "Ku ajiye wa kanku dukiya cikin Sama inda..., ɓarayi ba su hudawa su yi sata, gama wurin da dukiyarku ta ke can zuciyarku za ta kasance kuma" (Matta. 6:19-21).

Achan da gidansa suka halaka sabo da ya ke son zinariya, da azurfa, da tufafi masu daraja. Ya saci la'antaccen kaya (Josh. 7). Yahuda Iskariyoti kuma, almajirin Yesu, ya halaka don ya fi son kuɗi da Yesu (Matta. 27:3-5).

Copyright ANGP

**8.** **Shaiɗan** – A tsakiyar siffa ga Shaiɗan. Ba mu san kamannin Shaiɗan ba, amma sabo da mugun halinsa a kan siffanta shi kamar dabba mai ban tsoro. Shi ne uban maƙaryata duka. Shi ne makyayin namomin nan waɗanda muka rubuta labarinsu duka. Shi ne mai mulkin zuciyar mai zunubi. Yesu ya ce, "Ku na ubanku Shaiɗan ne, ƙyashe kyashe na ubanku kuma kuna da nufi ku yi. Shi mai kisan kai ne tun daga farko, bai tsaya a kan gaskiya ba, domin babu gaskiya a cikinsa. Sa'ad da ya ke yin ƙarya don kansa ya ke yi, gama maƙaryaci ne shi, da uban ƙarya kuma (Yoh. 8:44).

**9.** **Tauraro** – Tauraro ya zama misalin lamiri, watau murya wadda ta ke cikin zuciyar ko wane mutum, ta kan dami mutum idan ya yi zunubi. Amma a siffan nan, tauraro baƙi ne, watau zunubi ya ɓata shi har ba ya kan cika aikinsa sosai (Ibr. 10:22).

**10.** **Ido** – Idon Allah ko ina ya ke. Yana ganin kome da ke cikin zuciyar mutum. Babu abin da ya ke ɓoye daga idon Allah mai haske. Sabo da haka Allah ya san dukan asirai da tunanin zuciya, da nufe-nufenta. Ko ka yi mugunta cikin duhun dare, ko cikin baƙin jeji, ko cikin rami mai zurfi, ko ina inda ka ke Allah yana gani, dalilin ido ke nan.


**11.** **Mala'ika** – Mala'ika ya zama misalin Maganar Allah. Ba mu san kamannin mala'iku ba, amma mutane sun saba yi musu siffa irin wannan don su ne manzannin Allah. Allah yana magana da ruɗaɗɗen mai zunubin, yana roƙonsa ya tuba, ya yarda hasken Allah ya shiga zuciyarsa mai duhu. Kai ma Allah yana magana da zuciyarka ta wurin wannan littafi.

**12.** **Kurciya** – Wannan tsuntsu mai tsabta, marar ɓarna, mai son mutane ne, ya zama misalin Ruhu Tsattsarka, watau Ruhun Gaskiya, da ya ke soke zuciya a kan zunubi, da adalci, da shari'a. A cikin

wannan siffa Ruhu Tsattsarka daga waje ya ke, ba cikin zuciya ba. Ba ya iya zama inda zunubi ya ke yin mulki.

13. **Harsunan Wuta** – Abubuwan nan da su ke a kewaye da zuciya, harsunan wuta ne. Sun zama misalin ƙaunar Allah da ta ke kewaye da zuciyar mai zunubi. Allah ba ya son halakar mai zunubin, amma yana so ya tuba ya rayu. Yesu ya zo domin ya ceci masu zunubi. Akwai murna mai yawa a Sama bisa kan mai zunubi guda ɗaya wanda ya tuba. Allah yana so ya tsarkake zuciya cikin jinin Ɗansa, haifaffe shi kaɗai, Yesu Almasihu. Waɗannan harsuna sun zama misali, Yesu mai ƙauna ne. Ƙaunar Allah tana so ta shiga zuciyan nan mai sanyi, matacciya. Yesu yana tsayawa a bakin ƙofar zuciyarka yana salama. Idan ka yarda ka buɗe masa, zai shiga, ya tsarkake zuciyarka ya fisshe ka daga bautar Shaiɗan.

## 2. ZUCIYAR MAI TUBA




Wannan siffa misali ne na wanda ya soma tuba ya juyo ga Allah. Mala'ika yana riƙe da takobi, watau Maganar Allah wadda ke mai rai, mai aikatawa kuma, ta fi ko wane takobi mai kaifi biyu ci, tana kuwa hudawa har ta raba rai da ruhu, da gaɓaɓuwa da ɓargo kuma, tana kuwa da hanzari ga ganewar tunanin zuciya da nufe-nufenta (Ibr. 4:12). Maganar Allah tana tuna mana alhakin zunubi mutuwa ne (Rom. 6:23), kuma an ƙudurta wa mu ane su mutu sau ɗaya bayan wannan kuma shari'a (Ibr. 9:27). Rabon mai zunubi da marar ban gaskiya a cikin ƙorama mai ƙonewa da wuta ya ke.

A cikin wancan hannun mala'ika kuma, ga ƙwaƙwalwar mataccen mutum. Tana tuna mana ko wannemmu zai mutu. Jikin nan namu da mu ke ƙaunarsa ƙwarai, ga shi, muna sa masa ko wane irin tufafi, muna kiwonsa ƙwarai, muna yin kome don jikin nan ya ji daɗi, muna ciyad da kwaɗayinsa, amma ga shi zai mutu har ya ruɓe. Tsutsotsi za su cinye shi, amma dole ne rai da ruhu za su tsaya a gaban dakalin shari'a na Allah. Mai zunubin nan ya soma saurara ga Maganar Allah mai ban al'ajabi, yana kuwa buɗe zuciyarsa yana karɓar ƙaunar Allah. Ruhu Tsattsarka ya fara haskakawa cikin

zuciyarsa. Hasken Allah ya fara shiga sai duhu ya soma watsewa. Ƙaunar Allah mai daɗi ta shiga maimakon ɗacin nan na zunubi. Namomi duka, watau su zunubai, suna gudu.

Ka mai zunubi, sai ka yarda Yesu wanda ya ke hasken duniya ya shiga cikin zuciyarka, sa'an nan duhu da ayyukan duhu dole su bar zuciyarka, kamar yadda ka ke gani a cikin siffan nan. Yesu ya ce, "Ni ne hasken duniya, wanda ya ke biyo na ba zai yi tafiya cikin duhu ba." (Yoh. 8:12). "Kaiton waɗanda suka fi son duhu da haske." A lokacin da Yesu ya shiga haikali ya kori dukan masu sayar da shanu da tumaki da kurciyoyi, ya zubar da kuɗin masu yin canji ya ce, "Gidana gidan addu'a ne, amma kun maishe shi kogon mafasa" (Yoh. 2:13-17). Zuciyarka ita ce gidan nan. Yesu ya zo ba domin ya gafarta mana zunubammu kaɗai ba, amma domin ya cece mu daga kon zunubi, ya fisshe mu kuma daga mulkinsa. Idan fa Ɗan zai 'yantad da ku kwā zama 'yantattu da gaske (Yoh. 8:36).

## 3. ZUCIYAR MAI BA DA GASKIYA



Nan ne muna ganin zuciyar wanda ya yi tuban gaske. Yana ƙyamar zunubansa waɗanda suka sa Yesu ya mutu bisa giciye. Yana kallon giciye wanda mala'ika, watau Maganar Allah, ke nuna masa, har ya zub da hawaye don tausayi. Ƙaunar Allah da ke cikin Almasihu Yesu ta shige shi. Sai ka ce zuciyarsa za ta narke tum ba lokacin da ya ke tuna da Yesu Almasihu ba, shi wanda ke Ɗan Rago na Allah, wanda ya zo ya ɗauke zunubansa, ya mutu maimakonsa kuma a bisa giciye. Yana tunani yadda aka yi wa Yesu bulala, aka naɗa masa rawani na ƙayayuwa, aka buga ƙusoshi a cikin tafin hannuwansa da ƙafafunsa, an rataye shi a bisa giciye sabo da zunubammu. Har ya zamana sai ka ce zuciyarsa za ta karai. Yana karatun Maganar Allah, yana ganin kansa a cikin madubin Allah, yana gane yadda zuciyarsa ta ke, baƙa ce don zunubai. Ganin wannan yana sukan zuciyarsa. Ruhunsa mai tuba yana yin baƙin a kan zunubansa, har ya yi hawaye. Allah yana jawo shi kusa gare shi. Ƙaunar Allah da kwanciyar rai sun shiga zuciyan nan. Jinin Yesu Almasihu ya tsarkake ta daga dukan zunubai. Yanzu ya san abin da aka rubuta, "Ubangiji yana kusa da masu ƙaryayyar ziciya, yana ceton irin waɗanda su ke da ruhu mai tuba" (Zab 34:18). Yana warkad da masu ƙaryayyar zuciya, yana ɗaure miyakunsu (Zab. 147:3). Maganar Allah ta ce kuma, "Da wannan mutum zan kula, shi wanda ya ke talaka mai ƙaryayyen ruhu" (Ish. 66:2).

Ruhu Tsattsarka da ƙaunar Allah suna mulki cikin zuciyan nan da aka tsarkake. Mutumin yana dogara ga giciyen Yesu, da jinin da ya bayar domin a shafe zunubansa, sai ya fahinta, ashe, an gafarta zunubansa, a cikin zuciyarsa ya tabbata jinin Yesu Ɗan Allah yana tsarkake shi daga zunubi duka (1 Yoh. 1:7). Wanda ya ke ba da gaskiya ga Yesu ba zai halaka ba, amma ya sami rai na har abada (Karanta 1 Kor. 6:10,11). Muna da fansarmu a cikin Yesu ta wurin jininsa, da gafarar laifofimmu, gwargwadon wadatar alherinsa (Afis. 1:7). Yanzu akwai sabon Ruhu a cikin zuciyarsa. Daga nan gaba ba ya ƙaunar duniya da abubuwan da su ke a duniya, amma yana marmarin al'amuran Allah wanda ya cika zuciyarsa da ƙauna. Yanzu namomin, watau zunubansa daga waje su ke, amma Shaiɗan yana waiwayawa, ko da ya ke a waje ya ke, duk da haka yana so ya sami hanya ya koma ciki. Sabo da haka aka ce mu yi tsaro, mu yi addu'a, mu yi tsayayya da Shaiɗan, zai kuwa gudu (Yak. 4:7).

## 4. GICIYAYYE TARE DA ALMASIHU




Wannan siffa ta zama misalin mai bi wanda ya sami cikakken kwanciyar rai da fansa ta wurin hadaya ta Ubangiji Yesu Almasihu Macecimmu. Yana fariyar giciyen Yesu, wanda aka giciya masa duniya ta wurinsa, shi kuma an giciye shi ga duniya (Gal. 6:14). Ya gane sosai Yesu ya mutu bisa giciye dominsa kuma shi ya mutu ga zunubai, amma ya rayu ga adalci (1 Bit. 2:24). Mai bi giciyayye ne shi ga duniya. An dokace mu mu yi tafiya bisa ga Ruhu, kada kuma mu bi sha'awoyin jiki (Gal. 5:12-25). An rubuta kuma mu nemi tsarkakewa wadda babu mutumin da zai ga Ubangiji im ba tare da ita ba (Ibr. 12:14). A cikin wannan siffa wajen hagu ga gungume inda suka ɗaure Yesu da sarƙa bayan da suka tuɓe masa tufafinsa. Kuna ganin bulala kuma da suka buge shi da ita, horon da ya yi daidai mu mu samu, ya faɗo masa (Ish. 53:4,5). Aka bubbuge shi domin zunubammu. Sarki Hirudus da mutanensa suka yi masa ba'a. Bayan da suka yi masa bulala kuma suka sa masa rigar shunayya. A lokacin suka yi rawani na ƙayayuwa kuma suka naɗa masa maimakon rawanin zinariya irin da a kan sa wa sarakuna. Suka sa kara a hannun damansa kuma maimakon kandirin sarauta.

Suku durƙusa a gabansa, suka yi masa ba'a cewa, "A gaishe ka, Sarkin Yahudawa". Suka tofa masa yau, suka karɓi karan suka buge shi a ka. Bayan da suka gama yi masa ba'a suka kai shi wurin da za su giciye shi.

Yanzu fa, akwai mutane da yawa waɗanda su ke ce da kansu masu bi, suna kuwa yin addu'a a cikin majami'u. Suna cin jibin Ubangiji, suna rera waƙoƙin Allah, amma ta wurin ayyukan da su ke yi suna giciye Macecinsu sau na biyu kuma. In ji Yesu, "Ba dukan mai ce mini Ubangiji, Ubangiji, zai shiga cikin mulkin Sama ba, sai wanda ke aikata nufin Ubana wanda ke cikin Sama" (Matta. 7:21-27). A cikin siffar kuma ana ganin burgamin kuɗi na Yahuda. Yahuda ya ba da Yesu a bakin azurfa 30, domin ƙaunar kuɗi ta makantad da shi, ta kama zuciyarsa mai son mugunta. Ga kuma fitila, da sarƙa, da sauran kayan mayaƙan da suka kama Yesu da su da dare. Ga kuma lidon da mayaƙa suka yi caca da shi a lokacin da suka raba tufafin Yesu. Sun fa cika annabcin da ya ce, "Suna rarraba tufafina a tsakaninsu, a bisa rigata kuma suna jefa kuri'a." (Zab. 22:18).

Ga mashi kuma da mayaƙi ya soki haƙarƙarinsa da shi, jini da ruwa fa sun zuba (Yoh. 19:33-37). Tun zakara bai yi cara ba Bitrus ya yi musun Yesu a gaban budurwa, amma daga baya ya tuba da kuka da hawaye. Kaifa? Kana shaida Yesu ta wurin maganarka da ayyukanka? Ko kuwa kana tsoron shaida Yesu? Yesu ya ce, "Wanda zai yi musun sanina a gaban mutane, shi zan yi musunsa a gaban Ubana wanda ke cikin Sama kuma." (Matta 10:32-33). Yesu ya ce kuma, "Idan ko wane mutum yana da nufi ya bi bayana sai ya yi musun kansa, ya ɗauki giciyensa, ya biyo ni" (Matta 16:24) "kuma, wanda bai ɗauki giciyensa ya bi bayana ba, bai isa ni ba" (Matta 10:38).

Yesu Dutsen cetona,
Bar im ɓoye wurinka,
Jini–fansar zunubai,
Ruwa–tsarkakewar rai,
Ga su suna zubowa
Daga cikin zuciyarka.

Copyright ANGP

## 5. HAIKALIN ALLAH

A wannan siffa mun ga mai zunubin da aka tsarkake shi, an keɓe shi kuma ta wurin jin ƙan Allah da alherinsa. Yanzu zuciyan nan ta zama gidan Allah da gaske. Allah ba da Ɗa, da Ruhu Tsattsarka ke zaune a ciki, kamar yadda Yesu ya faɗa mana cewa, "Idan mutum yana ƙaunata, zai kiyaye maganata, Ubana kuwa zai kaunace shi, muzo wurinsa, mu yi zamammu tare da shi" (Yoh. 14:23). Allah yana sa wa mutumin albarka, yana ɗaukaka shi ta wurin Yesu Almasihu (Lk. 1:52).

Yanzu zuciya ta zama gidan Allah Mai Rai. An kawar da zunubi. Yanzu ba mu ganin namomin nan da Shaiɗan uban ƙarya, ke mulkinsu, amma muna ganin Ruhu Tsat, tsarka yana zaune a cikin zuciya. Maimakon ayyuka na jiki waɗanda suka zama da ban ƙyama, zuciya ta zama kamar lambu mai ba da amfani, ko itace mai ba da 'ya'ya, tana kuwa ba da 'ya'yan Ruhu, su ƙauna, da farin ciki, da kwanciyar rai, da tsawon jurewa, da nasiha, da nagarta, da aminci, da tawali'u, da kamewa, da irin waɗannan masu dacewa, ko ga Allah, ko ga mutum. Yanzu ya zama reshe mai ba da amfani a cikin itacen inabi na gaskiya, watau Ubangijimmu Yesu Almasihu. Asirin samun amfani haka, shi ne mutum ya zauna cikin Yesu Almasihu, Almasihu kuma ya zauna a cikinsa (Yoh. 15:1-10). Yana kuma kiyaye Maganarsa a zuciyarsa. Tun da aka cika shi da Ruhu Tsattsarka an kuwa yi masa baftisma ta wurin Ruhu, yana da iko ya ci nasara a kan jiki da kwaɗayinsa, yana giciye jiki da sha'awoyinsa. Ta wurin ikon Ruhu Tsattsarka yana da ikon "tafiya bisa ga Ruhu". Yanzu yana rayuwa ba bisa ga abin da ya ke ji, da abin da ya ke gani ba, amma bisa ga ban gaskiya. Ban gaskiya ga Yesu ita ce nasara wadda ta ke cin duniya. Yana rayuwa kuma ta wurin bege. Begen saurin komowar Ubangiji Yesu Almasihu ya kan ƙarfafa shi. Yana rayuwa kuma ta wurin ƙaunar Allah, wadda ke dauwama har abada.




Masu albarka ne masu tsabtan zuciya, gama su za su ga Allah (Matta 5:8). Dawuda sarki ko da ya ke mawadaci ne, ko da ya ke ya ci nasara a kan magautansa, ya kuma kashe Goliath da waɗansu, duk da haka ya sani akwai bukata ɗaya gare shi, wadda ta zama masa dole in zai ga Allah. Ya yi kuka tun daga cikin zuciya, ya ce, "Daga cikina ka halicci zuciya mai tsabta ya Allah, ka sabonta daidaitaccen ruhu daga cikina" (Zab. 51:10). Babu wanda ya iya tsarkake zuciyar kansa, ya sa zuciya mai tsabta cikinsa ta wurin ƙoƙarin kansa. Sai dole ya zo gun Allah ya yi tuban gaske, ya faɗi zunubansa, ya rabu da su kamar yadda Dawuda sarki ya yi. Ya yi kuma kamar ɓataccen ɗa wanda ya bar kiwor aladu ya dawo wurin ubansa da zuciya mai tuba, ya ce, "Ubana na yi zunubi a gaban Sama, a gabanka kuma." Allah zai yarda ya karɓi ko wane mai zunubi wanda ya yi tuban gaske. Allah ya yi alkawari cewa, Sabuwar zuciya kuma zan ba ku, sabon ruhu kuma zan sa a cikinku, daga cikin jikinku kuma zan amshe zuciyan nan ta dutse, in sa Ruhuna a cikinku, im bi da ku cikin farillaina.

A cikin wannan siffa mun ga mala'ika ya komo kuma. Mala'iku suna yi wa magadan rai na har abada hidima, suna kuwa kafa sansani a kewaye da masu tsoron Ubangiji (Zab. 34:7; 91:11; Dan. 6:22; Matta 2:13; 18:10; A.M. 5:19; 12:710). Ana kuma ganin Shaiɗan kusa da zuciya, yana neman hanyar komowa cikin gidansa na dā. Sabo da haka aka ce mu yi tsaro, mu yi addu'a domin magaucimmu, Shaiɗan, kamar zaki mai ruri yana yawo, yana neman wanda zai cinye (1 Bit. 5:8). Ku yi tsayayya da Shaiɗan, zai fa guje muku (Yak. 4:7).

Copyright ANGP

## 6. ZUCIYAR MAI SHAKKA




Wannan siffa misali ne na wanda ya ja da baya, abin baƙin ciki ne. Ido ɗaya ya soma rufewa, yana son barci, watau zuciya ta yi sanyi. Wancan ido ɗayan kuma yana kallon sha'awoyin duniya, yana nemansu, ba kunya. Haske yana ragewa daga cikin zuciyarsa. Alamomin nan masu nuna shan wahala na Yesu sun yi barkatai, ba su kuwa tsaya sosai ba. Yau da gobe jarabur da ke kewaye da shi suna cin nasara. Ba ya yin tsayayya da Shaiɗan. Yana sauraron muryar Shaiɗan, ba muryar Allah ba. Har yanzu yana zuwa majami'a, yana ɓoye son duniya da ke cikin zuciyarsa, amma yau da gobe yana ƙara nisa da Allah. Ya bar ƙaunar Allah da ya yi da fari. Tauraron cikin zuciyarsa, watau muryar Allah, ba shi da haske yanzu. Giciye ya zama kaya mai nauyi a gare shi. Ya fara zuciya biyu, ya bar yin addu'a kuma. Ba ya tsaron zuciyarsa sosai, yana ba Shaiɗan wuri. Aljan nan na kwaɗon yana neman hanyar shiga. Mutumin ya zama mai girman kai. Watakila yana girman kai a kan bin da ya ke yi, yana mantawa an cece shi ta wurin alherin Ubangiji kurum. Jarabar shan giya tana damunsa. Watakila dai wani ɗanuwansa yana roƙonsa ya taɓa sha kaɗan kawai, ko kuwa ana ce masa wata irin giya ba ta da ƙarfi. Bai sani ba, shan giya kaɗan ita ce ƙaramin rafin da ke gangarawa zuwa babban kogin mai hauka. Ko kuwa wata mace tana dafa wa mijinta da abokansa giya,tana kawo hujja, wai ita da kanta ba ta sha. Amma tun da ta ke jawo waɗansu ta sa su su sha, ita da kanta ta ruɗe da wannan zunubi. Shaiɗan, mai wayo, yana jarabar masu bi da fasikanci da zina. Watakila kuwa ya soma sauraran gautsin baki da ƙazanta, yana kuwa jin daɗin yawo tare da 'yan duniya, yana tafiya wurin wasanni da kiɗe kiɗe da raye raye na duniya. Am faɗa masa wai rawa irin ta Turawa, watau namiji da mace suna rawa tare, ba zunubi ba ne, sai rawar arna. Amma bai sani ba, rawa ta ko wace iri uwar fasikanci ce, har ma irin wadda Turawa su ke yi ta fi muni. Shan sigari da shan tabar Turawa da tabar baƙar fata duka ɗaya ne har ma Turawa masu sha sun cika sha ainun. Su kan wuni suna sha, su kwana suna sha. Yesu bai taɓa shan taba ba, masu binsa kuwa ba su yi.

Shaiɗan yana cewa yin wasa da zunubi, ba zunubi ba ne. A yi zunubi sau ɗaya, a yi aikin ƙazanta sau ɗaya, ba laifi ne ba. Ta haka mai jaraba ya kan riƙa ruɗin mutum, har ƙazantaccen aljanin fasikanci ya sami hanyar shiga cikin zuciyar da aka wanke.

Cikin siffar mutumin da ke sukan zuciya da wuƙa shi ne misalin masu ba'a da su ke yi wa masu bin hanyar Yesu tsegumi. Mai bin nan yanzu bai iya haƙurin ba'a da baƙar magana da a ke yi masa ba, balle fa ba'a daga wurin abokansa. Maganarsu ta kan soke zuciyarsa, tun da ya bar ƙaunarsa ta fari, ya

Copyright ANGP

soma tsoron mutane fiye da Allah. Sabo da yana tsoron mutane, ya zama bawan mutane, ya ƙara ja da baya ke nan.

Fushi da hasala sun shigo lokacin da ya ke shan wuya ko wahala, suna so su yi mulkin zuciyarsa kuma. Rantsuwa da zagi su kan ƙazantad da bakinsa wanda ya kan yabi Allah, ya kan yi addu'a da shi kuma. Idan Shaiɗan ya sami ƙofa ƙanƙanuwa zai shigad da kishi, ya ƙara buɗe ƙofa don waɗansu zunubai kuma.

Son kuɗi kamar ɓarawo ne, ya kan yi wa zuciya sanɗa. Ba wuya ya shiga idan ba mu saurari maganar Yesu ba, da ya ce, "Ku yi tsaro, ku yi addu'a, kada ku shiga cikin jaraba" (Matta 26:41). Domin wannan fa wanda ya ke mai da kansa yana tsaye, ya yi lura kada ya faɗi (1 Kor. 10:12). Dole ne ku yafa dukan makamai na Allah domin ku sami iko da za ku yi tsayayya da dabarun Shaiɗan (Afis. 6:11-18).

## 7. ZUCIYAR MAI JA DA BAYA




Wannan siffa tana nuna mana yadda zuciya ta ke ta wanda aka haskaka shi sau ɗaya, ya ɗanɗana baiwar Almasihu, aka ba shi tarayya kuma cikin Ruhu Tsattsarka, amma daga bisani ya ja da baya. Yohanna ya ce, " 'Ya'ya ƙanƙanana, sa'a ta ƙarshe ke nan: kamar yadda kuka ji magaucin Kristi yana zuwa, ko yanzu magautan Kristi da yawa sun taso; sabo da wannan mun sani sa'a ta ƙarshe ke nan.

Suka fita daga cikimmu, amma ba na cikimmu ba ne; gama da namu ne, da suka lizima tare da mu: amma suka fita, domin su bayyanu su duka ba namu ba ne" (1 Yoh. 2:18,19). Ya kuma zama misalin zuciyar wanda bai taɓa tuba ba. An yi masa wa'azi, ya ji, amma ya taurare zuciyarsa, bai bar yin zunubansa ba.

Yesu da kansa ya bayyana yadda zuciyar marar tuba ta ke, ya ce, "Kazamin ruhu lokacin da ya fita daga cikin mutum, ya kan bi ta cikin wurare marasa ruwa, yana neman hutawa. Da bai samu ba, sai ya ce, "Na koma gidana inda na fito." Sa'ad da ya iso, ya iske shi sharарre ne, gyartacce ne kuma. Sai ya tafi ya ɗauko waɗansu ruhohi bakwai waɗanda suka fi shi mugunta, su shiga su zauna a wurin.

Karshen zaman wannan mutum ya fi na fari mugunta (Lk. 11:24-26). Ya zama gare su bisa ga karin maganan nan mai gaskiya, kare yana komawa zuwa wajen haraswa tasa, gursuna wadda ta yi wanka kuma ga birkiɗa cikin lāka (2 Bit. 2:22).

Waɗannan nassoshi suna bayyana sosai yadda zuciyar mutumin nan ta ke. Zunubi mai cutarwa ya zo don ya zauna, ya yi mulkin zuciya. Ko a fuskarsa ana ganin alamar ruɓewar da ke cikin zuciyarsa. Ruhu Tsattsarka ya tashi, don zunubi da Ruhu Tsattsarka ba su zaunuwa gida ɗaya. Haske da duhu ba su gamuwa. Ba shi yiwuwa zuciya ta zama gidan Allah, da na Shaiɗan gaba ɗaya. Mala'ika, watau Maganar Allah, ya tafi da baƙin ciki. Yana waiwaiyawa ya gani ko mutumin zai tuba kamar ɓataccen ɗa wanda ya koma cikin hankalinsa tun yana zaune wurin aladu, yana son ya ci dusar da aladu ke ci, amma ba wanda ya ba shi. Ya tuna yadda ya ke, ɓatacce ne, ya tuba ya ce, "In tashi in tafi wurin ubana, in ce masa, na yi zunubi gaban Sama, da kuma gabanka, ban isa ba a ƙara ce da ni ɗanka." Sabo da tuban gaskiya da ya yi, da kuma baƙin ciki a kan zunubansa, uban ya gafarta masa ya yanka ɗan maraƙi kiyayayye, ya karɓe shi tare da murna da farin ciki.

Amma wannan mutum ba ya son irin tuban da zai kawo shi ga Allah, har ya fāɗi a gaban Yesu ya roƙi gafara da tsarkakewa. An yi wa lamirinsa lalas sai ka ce da ƙarfe mai wuta, an kashe. Yanzu yana da kunne na ji, amma ba ya jin muryar Allah. Yana da ido, amma ba ya ganin rami marar matuƙa inda zai faɗa bayan an jima kaɗan. Ba shi da kunya, ba shi da ladama yanzu, yana zunubi a fili. Shaiɗan ya shiga zuciyarsa, ya hau gadon sarauta. Watakila daga waje har yanzu mutumin yana taƙamar kyaunsa, amma ya zama kamar kabarin da ka shafe shi da farar ƙasa, amma daga ciki cike ya ke da ruɓaɓɓun ƙasusuwan matattu da ƙazantar zunubi (Matta 23:27). Uban ƙarairayi ya shiga maimakon Ruhun gaskiya. Ko wane nama, watau su zunubai, sai ka ce yana da nasa aljanin da zai taimake shi mulkin zuciya. Ko da ya ke so ya fita daga hannun ƙazaman ruhohin nan, masu gwada masa azaba, bai iya ba. Ya zama bawansu. Ya zama masa kamar yadda Allah ya ce, Mutum wanda ya waƙala shari'ar Musa yana mutuwa. Ina misalin fikon zafin hukunci ga tsammaninka da za a aza wa wanda ya tattake Ɗan Allah ƙarƙashin sawunsa, ya mai da jinin alkawari wanda aka tsarkake shi da shi, abu marar tsarki, ya rena Ruhu na alheri (Ibr. 10:28-31; 2 Bit. 2:1-14).

Mai karatu! Idan haka zuciyarka ta ke, sai ka yi kuka mai zafi a gaban Allah. Yana da iko, zai fa yarda, ya cece ka, ya gafarta maka, ya tsarkake ka daga dukan zunubanka idan za ka zo ka tuba da gaske. Yana da iko ya ɗaure Shaiɗan da mataimakansa duka, ya fisshe su daga zuciyarka, idan dai ka yarda. Zo kamar kuturun nan wanda ya zo gaban Yesu ya kuwa ce, "Idan ka yarda, kana da iko ka tsarkake ni." Yesu ya ce, "Na yarda, ka tsarkaka" (Mk. 1:40-43). Amma idan kana ƙara taurara zuciyarka, kana fin son duhu da haske, babu dama, ba mai taimakonka. Ka zaɓi mutuwa a maimakon rai, duhu a maimakon haske kuma.

Copyright ANGP

## 8.MUTUWAR MAI ZUNUBISIFFA TA TARA

A nan muna ganin mai zunubi, da zuciyarsa tattaura, yana bakin mutuwa, jikinsa yana cikin azaba, ransa cike ya ke da tsoron mutuwa. Mutuwa (watau jikin nan mai ƙasusuwa zalla) ta zo masa ba labari ba ya kuwa son zuwanta. Tana yi masa mugun dubi da idonta marasa jin tausayi, mai ban tsoro. Daɗin yin zunubi ya ƙare. Yanzu ya fara samun alhakin zunubi mai wuya. Ya firgita.

Azabar Gidan Wuta ta kama ransa da ruhunsa. Watakila yana son yin addu'a, amma addu'arsa banza ce. Allah bai yarda ba. Maganar haƙuri da abokansa ke yi masa banza ce. Wadatarsa da ya tara, ba ta cetonsa, ba ta sauƙaƙe ciwonsa, ba ta kuwa iya ƙara masa kwanaki. Yana so ya yi tunani a kan Allah, amma Shaiɗan ya hana. Dukan annashuwa ta duniya da abin da ya ke jin daɗinsa a dā, yanzu sun zama banza. Malamansa da ya ke dogara gare su ba su iya taimakonsa. Yanzu ya sani abin tsoro ne a faɗa cikin hannun Allah Mai Rai.

Dā cewa ya ke yi idan mutuwa ta kusance shi, zai tuba, amma yanzu bai iya ba. Mutane dubbai su kan yi mutuwar kadangatse, ba su da damar tuba, ko da ya ke suna so. Sabo da haka aka ce, "Ku nemi Ubangiji tun yana samuwa."




A maimakon jin Maganar Allah mai ta'aziyya, wannan mai zunubin ya ƙi alherin Allah da ƙaunarsa tun yana da lafiya, yanzu zai ji muryar Alƙali cewa, "Ku rabu da ni ku la'antattu zuwa cikin wuta ta har abada wadda aka shirya wa Shaiɗan da mala'ikunsa" (Matta 25:41). An ƙudurta wa mutane su mutu sau ɗaya, bayan wannan kuma shari'a (Ibr. 9:27).

Copyright ANGP


**9.ZUCIYAR MAI YIN NASARA**

Nan mun ga misalin mai bi na gaske wanda ya ke haƙuri yana cin nasara a kan wahala da jaraba da Shaiɗan ya kan yi masa, da sha'awoyin jiki kuma. Ana yi masa jaraba da yawa, amma ya jure har matuƙa. Ya fi gaban mai nasara ta wurin Yesu Almasihu. Bai fara yin tsere kawai ba, amma ya ƙure fage, yana zuba ido ga Yesu shugaban ban gaskiyarmu (Ibr. 12;1-2).

Shaiɗan da dukan rundunansa sun kewaye zuciyar mai ba da gaskiya. Suna ta neman hanyar shiga, amma babu dama. Girman kai, da son kuɗi, da ruhun fasikanci suna son shiga. Ga bunsuru da jaki a maimakon karen da damisa. Watau zunubi ya kan yi rikiɗa don ya ruɗi mai bi. Amma mai bi wanda ya yi tsaro, zai san zunubi, kome rikiɗewarsa, ko da ya zo da kamar mai addini ne, ko kamar mala'ikan haske, ba zai yarda da shi ba. Maganar Allah da Ruhun Gaskiya da ke cikin zuciyarsa suna bi da shi cikin dukan gaskiya, suna taimakonsa ya gāne bambancin nagarta da mugunta.

Tare da namomi masu yawa da aljannunsu, ana ganin wani mai rawa da ƙoƙon giya a hannunsa. Yana yi wa mai bi jaraba da sha'awoyin duniya, da shan giya, da rawa. Amma wannan duka banza ne ga mai bi wanda ya ƙebe kansa ga Allah. Ya mutu ga duniya da zunubi. Jaraban nan dai ta kan sa ya matsa kusa da Allah. Ga wani mutum kuma da ya ke sukansa da wuƙa. Marasa ban gaskiya, har waɗansu da su kan ce da kansu masu bi suna sukansa da tsegumi, da zagi, da ba'a. Su kan yi masa tsanani kuma. Amma yana tunawa da maganar Yesu cewa, "Masu albarka ne ku lokacin da a ke zarginku, ana tsananta muku, da ƙarya kuma ana ambatonku da ko wace irin mugunta sabili da ni. Ku yi farin ciki ku

yi murna ƙwarai, gama ladanku mai girma ne cikin Sama” (Matta 5;11-12). Zunubi, da halin nan na jiki, da na son kansa, da Shaiɗan duk suna ƙoƙari su raba mai bi da ƙaunar Allah. Amma gaba gaɗi mai bi




yana cewa, “Wa zai raba mu da ƙaunar Kristi? ko ƙunci, ko raɗaɗi, ko tsanani, ko yunwa, ko huntanci, ko haɗari, ko takobi? Labudda, cikin dukan waɗannan al’amura mun fi gaban masu nasara ta wurin wanda ya ƙaunace mu” (Rom. 8:35-39). Tun da ya yafa dukan makamai na Allah ya iya tsaya a cikin ranar jaraba ta wurin ikon Ruhu Tsattsarka. Yana cin nasara a kan jiki da ko wace irin jaraba. Ya sani Almasihu wanda ya ke cikinsa ya fi Shaiɗan da rundunarsa iko. She wanda ya ke cikimmu ya fi wanda ke cikin duniya, watau Shaiɗan, iko. Yesu Almasihu ya ci nasara a kan Shaiɗan, da zunubi, da mutuwa. Ta wurinsa kuwa mun fi gaban masu nasara, za mu ci nasara, za a fa ba mu rawanin daraja.

Tauraro, watau lamiri, yana ta haskakawa. Zuciyarsa cike ta ke da ban gaskiya da Ruhu Tsattsarka. Mala’ika a bisa yana tuna masa alkawarai masu daraja don waɗanda ke cin nasara, suna kuwa dauwama har abada abadin (Ruya 2:7,11,17,26; 3:5;12;21).

Ga jakar kuɗi a buɗe. Watau ba zuciyarsa kaɗai ya buɗe ba, amma duk da kuɗinsa, da kome da ke gare shi, ya bayar don aikin Allah. Maimakon ɓata kuɗinsa a kan annashuwar duniya yana taimakon fakirai, yana ba da zakka ga Allah.Bayan da ya fid da zakka kuma yana bayarwa gwargwadon iyawarsa. Ko yaushe yana ba da kuɗinsa don ya girmama Allah, kamar saniya da ba ta hana wa mai ita madara. Dunƙulin gurasa da kifi suna nuna mana ciyeciyensa na kirki ne. Ba ya shan giya ko bammi. Ba ya cin naman da aka yanka wa gunki, ba ya cin mushe. Ba ya shan taba, don ya tuna jikinsa haikalin Allah ne, yana riƙonsa da tsarki. Zuciyarsa ta zama gidan addu’a, amma wannan ba zai hana masa taruwa a majami’a tare da masu bi ba, ko ana ruwa ko ana rana. Yana son addu’a ƙwarai ko cikin gidan addu’a ko cikin daƙinsa. Ko wace rana ya kan tara iyalinsa don addu’a ba fasawa. Idan mai bi ya bar yin addu’a ba ya rayuwa, ya zama kamar kifi wanda aka fisshe shi daga cikin ruwa shi ma ba ya rayuwa. Littafin da ya ke a nan a buɗe alama ce ya kan karanta Littafi Mai Tsarki kullum. Yana marmarin karatunsa, ya zama fitila ga ƙafafunsa, da takobi kuma wanda ya ke yaƙan Shaiɗan da shi. Maganar Allah ta zama masa cimaka ta ruhu, tana ciyad da ransa yau da gobe. Ta zama masa ruwan sha mai rai. Ta zama masa ruwan wanka kuma. Ta zama masa madubi inda ya ke ganin yadda zuciyarsa ta ke.

Mai bi yana jin daɗin ɗaukar giciye kuma. Yana tunawa yadda an giciye shi tare da Almasihu, ya fa tashi cikin sabon rai. Ya kan nemi abubuwan da ke bisa, watau abubuwan da ke dauwama har abada, ba abubuwan da a ke gani da ido yanzu ba. Ya kuwa shirya ya gamu da Allahnsa. Ya zama kamar itacen da aka dasa a magudanar ruwaye, wanda ya kan ba da ’ya’yansa a cikin kwanakinsa. Ya zama

Copyright ANGP

kuma kamar reshe cikin kurangar inabi mai gaskiya wanda ya kan ba da 'ya'ya da yawa. Cikakkiyar ƙaunar Allah ta cika zuciyarsa, sabo da haka ba ya tsoron mutuwa (Zab. 1:1-3; Yoh. 15:1-14; 1 Yoh. 4:18-21).

## 10. RASUWAR MAI BIN YESU




Yesu ya ce, "Ni ne tashin matattu, ni ne rai, wanda ya ba da gaskiya gare ni, ko ya mutu, zai rayu, kuma dukan wanda ya ke da rai yana kuwa ba da gaskiya gare ni, ba ya mutuwa har abada (Yoh. 11:25-26). Wanda ya ke jin maganata, yana kuwa ba da gaskiya ga wanda ya aiko ni, yana da rai na har abada, ba ya zuwa wurin shari'a, amma ya rigaya ya ratsa mutuwa zuwa cikin rai" (Yoh. 5:24). Mutuwa ba ta da ban tsoro ko azaba ga mai bi, don nasara ta haɗiye mutuwa. "Ya mutuwa, ina nasararki? Ya mutuwa ina ƙarinki? … Amma godiya ga Allah wanda ya ke ba mu nasara ta wurin ubangijimmu Yesu Kristi" (1 Kor. 15:54-57).

Wanda ya yi zumunta da Allah tun yana da rai ba ya tsoron mutuwa. In kwanakinsa sun cika zai tafi da murna zuwa ga madawwamin gidansa, a Sama. In ji Bulus manzon Allah, "Hankalina ya rabu biyu, ina da guri in tashi in zauna tare da Kristi, gama ya fi kyau ƙwarai" (Fil. 1:23). Mai bi yana marmarin ganin fuskar Yesu, wanda ya mutu sabo da shi a bisa giciye ya kuwa fanshe shi da jininsa. Ruhu Tsattsarka yana tuna masa maganar Yesu yadda ya ce, "Kada zuciyarku ta ɓaci, kuna ba da gaskiya ga Allah, ku ba da gaskiya gare ni kuma. A cikin gidan Ubana akwai wurin zama da yawa. …Sai in sake dawowa in karɓe ku wurin kaina, domin wurin da na ke, ku zauna kuma" (Yoh. 14:1-4). Ido bai gani ba, kunne bai ji ba, bai ko shiga zuciyar mutum ba, dukan iyakar abin da Allah ya shirya wa waɗanda ke ƙaunarsa (1 Kor. 2:9).Babu wani harshen mutanen duniya wanda ya iya fasalta, ko a bayyana darajar Gidan Allah wanda aka shirya wa waɗanda suka ci nasara a nan duníya, sun kuwa ba da gaskiya ga Yesu Almasihu.

Wannan siffa ta goma tana nuna mana mutuwar mai ba da gaskiya ga Almasihu. Maimakon jikin nan na ƙasusuwa, watau mutuwa, ga mala'ikan Allah. Yana jira ya ɗauki ruhun wanda ya barata ta wurin jinin Yesu, ya kai shi wurin Allah. A kan sāke ruhu da rai daga jikin nan inda suka zauna, sai ka ce fursuna ne. Su kan tashi su tafi zuwa wurin wanda su ke ƙauna, watau Yesu. Ko dā ma mai bi ya rayu abo da shi, da taimakonsa kuma ya ke zamansa a nan duniya. Can ana jiransa, a yi masa maraba a gaban Allah. Ubangijinsa zai ce masa, "Madalla, kai bawan kirki, mai aminci, …ka shiga cikin farin zuciyar Ubangijinka" (Matta 25:21). Shaiɗan ba shi da sauran iko bisa gare shi don "a ganin Ubangiji, mutuwar tsarkakansa aba mai daraja ce" (Zab. 116:15). "Na ji wata murya daga Sama ta ce, Ka rubuta,

Masu albarka ne matattu waɗanda ke mutuwa cikin Ubangiji daga nan gaba, in ji Ruhu, domin su huta daga aikace aikacensu, gama ayyukansu suna tafiya tare da su" (Ruya 14:13).

Kai, makaranci, Allah ya taimake ka, ka ba Yesu zuciyarka tun yanzu. Ya ce, "Dana (ko ɗiyata) ka ba ni zuciyarka." Zai ba ka zuciya mai tsabta. Zai sa daidaitaccen ruhu a zuciyarka. Kada ka bi sha'awoyin zuciyarka. Zuciyarka mai rikici ce za ta kai ka ga halaka. Wanda ya dogara ga zuciyar kansa wawa ne. Amma wanda ya taka a hankali za a cece shi (Mis. 28:26). Rabu da zunubanka, ka nemi adalci, don hakkin zunubi mutuwa ne, amma kyautar Allah rai na har abada ce cikin Yesu Almasihu Ubangijimmu (Rom. 6:23).

Ku fa waɗanda kuka ɗanka wa Allah rayukanku, ku kiyaye sahihiyar koyarwa cikin ban gaskiya da ƙauna wadda ta ke cikin Almasihu Yesu. Kun san wanda kuka ba da gaskiya gare shi, kun kuwa kawar da shakka yana da iko ya tsare ajiya da kuka ɗanka masa zuwa waccan rana. Ku gina kanku bisa ban gaskiya mafi tsarki, kuna addu'a cikin Ruhu Tsattsarka. Ku tsare kanku cikin ƙaunar Allah, kuna zuba ido ga Yesu shugaban ban gaskiyarmu da mai cikarta. Shi ne Sarkin Sarakuna, wanda mu ke duban zuwansa daga Sama ko yaushe.

Yanzu ga wanda ya ke da iko ya tsare ku daga yin tuntuɓe, ya sanya ku marasa aibi cikin mafificin farin zuciya a gaban bayyanuwar darajarsa, ga Allah Makaɗaici Macecimmu ta wurin Yesu Almasihu Ubangjiimmu, daraja da ɗaukaka da mulki da iko… yanzu da har abada abdin (Yah. 24 da 25).

Akwai ƙasa mai haske a can,
Shiryayya don duk masu bi,
Almasihu, Mai Ceto na nan,
Za mu gan shi tare da Uban.
Can akwai hutawa,
Daɗin hutu gun Yesu Mai Rai
Za mu zauna da shi
Cikin mulkinsa har abada.
Can akwai muna har abada,
Wurin Yes akwai kwanciyar rai,
Za mu manta da wahalan nan,
Wurin Yesu sai daɗi kaɗai.

Copyright ANGP

## A SPECIAL WORD FROM ANGP
## UN MONDE SPÉCIAL DE L'ANGP
## UMA PALAVRA ESPECIAL DA ANGP

**This booklet "The Heart of Man" is available in over 538 languages and dialects spoken throughout the world (Africa, Asia, The Far East, South America, Europe, etc.) Our Heart Book is now also available on cell phones, tablets, etc from www.angp-hb.co.za or as an APP "Heart of Man" on Android phones.**

**Le livre du "Coeur de l'homme" peut etre obtenu en plus de 538 langues et dialectes parles dans le monde entier, a savoir: Afrique, Amerique, Asie, Extreme Orient, Europe. Notre Livre du Coeur est maintenant aussi disponible sur votre Telephone cellular, plaques, etc. de www.angp-hb.co.za ou comme une Application "Heart of Man" sur telephones Android.**

**Este livro "O Coracao do Homem" e obtfdo em mais de 538 linguas e dialectos falados em todo o mundo, a saber: (Africa, Asia, America do Sul, Extremo Oriente, Europa, etc). O nosso Livro O Coração do Homem tambem esta agora disponivel em telefone celular, tablets, etc. de www.angp-hb.co.za ou como um aplicativo "Heart of Man" nos telephones celulares Android.**

**The 10 heart pictures contained in this booklet are also available in the form of large coloured picture charts (86 x 61cm) bound together in a set of 10 pictures. These "Heart Charts" can be obtained with European or African features and are particularly suitable to be used in conjunction with the Heart Book for class-teaching, open air evangelization etc. Kindly contact us to ascertain the latest subsidized price of this chart.**

**Les 10 images du coeur qui figurent dans ce livre peuvent etre obtenues en tableaux de couleur, format 86 x 61 cm, avec des physionomies europeennes ou africaines. Ils peuvent etre utilises en meme temps que le livre du coeur pour des classes bibliques, a l'ecole du dimanche ou lors de reunions de plein air. Soyez aimable de nous contacter pour assurer les derniers prix en cours du tableau.**

**As 10 imagens do coracao, contidas neste livro podem ser obtidas num conjunto de 10 imagens em colorido no tamanho de (86 x 61 cm). Estes "Cartazes do Coracao podem ser obtfdos com caracterfsticas Europeias e Africanas e podem ser usados em conjuncao com o mesmo livro em classes de ensino biblico, evangelizacao ou ao ar livre. Agradeciamos que nos contacta- se para confirmacao do ultimo preco dos cartazes.**

Copyright ANGP



**Kindly write to us if you are able to assist us with further translations of our free Gospel literature, informing us of the language into which you could translate this Gospel literature. Your assistance would be appreciated.**

**If you have found salvation in Christ, or have been otherwise blessed through our Gospel literature, please let us know. We would like to thank God with you, and remember you further in our prayers.**

**Nous vous invitons a nous contacter pour faire des arrangements concernant de nouvelles traductions de notre litterature, nous informant de la langue dans laquelle vous pouvez traduire cette litterature evangelique. Votre aide sera beaucoup appreciee.**

**Si vous avez trouve le salut en Christ ou si vous avez ete beni par notre litterature, nous vous prions de nous le faire savoir. Nous aimerions remercier Dieu avec vous et prier pour vous.**

**Nos vos convidamos a nos contactar, afim de fazer qualquer arranjo concernente a novas traducoes de nossa literatura em outras lfnguas. Vossa assistencia sera muito apreciavel.**

**Se tem encontrado a salvacao em Cristo, ou se tem sido abencoado por intermedio da nossa literatura evangelica, faca o favor de nos informar. Pois nos gostarfamos de agradecer a Deus juntamente convosco, e lembra-lo sempre em nossas oracoes.**

For free Gospel literature, books and tracts in over 538 languages, write to:

Pour obtenir gratuitement de la litterature evangelique, des livres et des traites en plus de 538 langues, ecrivez a:

Para obter gratuftamente a literatura evangelica, livros e folhetos em mais de 538 Ifnguas diferentes escreva para:


www.angp-hb.co.za

info@angp.co.za

**ALL NATIONS GOSPEL PUBLISHERS**
**P.O. Box 2191**
**PRETORIA**
**0001**
**R.S.A.**


**A Gospel Literature Mission financed by donations**
**Une Mission de litterature evangelique financee de dons**
**Missao de literatura Evanqelica financiada por donativos**

(Reg. No. 1961/001798/08)

**The "HEART OF MAN" books can be downloaded, viewed and saved using the following link:**

www.angp-hb.co.za

Copyright ANGP